Da kyar ta iya mikewa ta soma dafa bango, tana mikewar jini na tsinke mata. Daga nan sai wani duhu ya mamayi ganinta, ganinta ya dauke gaba daya ji ka ke yif! Ta fada a kan Fahimah da ke jan minshari sabida dadin A.C.

A firgice ta farka, ta janye Amrah daga kan kafafunta tana salati. Ta mike jiki na rawa ta kunna kwan lantarki. Nan ta ga jini na fita a jikin Amrah, kuma ko motsi ba ta yi. Fahimah saboda gigicewa a guje ta fita dakin Ammi tana kwala mata kira tun daga falo.

Hatta Baba Talatu da ke baskwata sai da ta jiyo kiran Ammi da Fahimah ke yi. Babban tsoronta kada a ce ta kashe matar Uwais. Cikin barci Ammi ke jiyo ihun Fahimah yana doso dakinta, don haka a bakin kofa suka ci karo. Fahimah ta hada hannayenta waje guda kasan habarta kamar mai roko. Ta ce,

"Ki taimaka Ammi, Amrah za ta mutu a dakina, wallahi ban mata komai ba. Kawai tashi nayi na ganta a kaina jini na zuba. Na shiga uku Ammi…".

Ammi ta ce, "Ke da Allah can shashasha, haihuwa ce".

Ta ture ta ta wuce dakin nata. Daidai lokacin da Baba Talatu ma ta karaso. A tare suka shiga dakin suna ganin halin da Amrah ke ciki suka gane wannan haihuwa ta zo da tangarda.

Ammi ta ce da Talatu maza dauko min wayata da mukullin mota".

Talatu da gudu ta juya ta dauko. Ammi da Talatu suka ciccibi Amrah suka yi waje. Ammi na cewa, Fahimah ta dauko jakar da Amrah ta zo da ita gaba daya ba za a rasa kayan jariri ba. Ta biyo su.

Asibitin Standard suka wuce don komai dare ba a rasa likita, suna zuwa aka karbe ta da gaggawa. Dubawa ta farko likita ta ce,

"Amrah ba za ta iya haihuwa da kanta ba an samu matsala mai girma, sannan babyn a breach yake, abu mai sauki shine CS kawai don su ceceta ko babyn, amma ita ko babyn dole a rasa guda.

Sabida tsananin rudewa Ammi kalmar shahada ta ke ja. Fahimah kuwa sai mazari ta ke daga tsaye. Likita ya ce maza mijinta ko mahaifinta su zo su sanya hannu don lokaci ya kure babu wani taimako da za su iya yi mata bayan CS.

Talatu ce mai karfin halin ce da Fahimah,

"Ba ni wayar Ammi da ke hannunki bayan kin latso min uban dakina".

Haka Fahima ta yi, ita mantawa shaf ta yi da wayar Ammi na hannunta don a gida ta baro tata. Ta lalubo lambar Uwais hannunta na karkarwa ta bai wa Talatu.

Bugu daya Uwais ya dauka don yana can kamar mai nakudar shima, yana jiran abin da zai biyo baya, me ya kawo Amrah gidansu har dakin Fahimah cikin dare haka, kuma ina Fahimar ta ke da ta barta ta daukar mata waya tsakar dare? Ya tabbata sha'ani ya lalace kam, da ya ji shawarar mahaifiyarshi tun farko da haka ba ta faru ba.

Yanzu da wane yare zai yi wa Amrah bayanin da za ta fahimce shi? Kuma me za ta dauki Fahimah? Ba za ta kara yarda da ita ba duk son da ta ke mata yau zai koma kiyayyah.

Talatu na kira yana dagawa, a nitse ta gaya masa halin da ake ciki da bayanin da likita ya yi. Uwais ji ya yi kamar kwarankwatsa ta fado a kansa, ya ji kamar ya yi fiffike ya ganshi a Nijeriya. Babynsa! Gudan jininsa da ya kwallafa wa rai yau ga kuskurensa zai yi sanadinsa.

"Ba ni likitar".

Kawai ya ce cikin tashin hankali.

Ya gaya mata ba ya kasar, sannan iyayenta ba sa gari, ya amince a yi mata CS din da duk wani taimako da ya dace. Ya kara da cewa,

"Likita ki taimake ni kada in rasa kowanne a cikin su. Don dukkansu ina so, and they mean a lot me. Kuma na yi mata laifi ina so in nemi gafarar ta… idan ta mutu a wannan halin bazan taba yafewa kaina ba.....".

Gaba daya muryarsa ta karye kamar ba Uwais ba. Bolded and courageous a komai. Likita bata tsaya doguwar magana dashi ba don ta lura ba'a hayyacin sa yake ba, suka shirya Amrah zuwa dakin tiyata.

******

"It's a baby boy, amma bai zo da rai ba. The mother is still unconscious, za ta dawo hayyacinta in the next two hours in allurar barci (anaesthesia) ta sake ta, sai ku shiga ku ganta".

Siririyar nurse din ta fadawa Ammi, a lokaci guda ta mika mata jaririn nannade cikin farin shawul. Ammi hannu da jiki na rawa ta amshe shi ta bude fuskarsa su duka ukun suka zuba masa ido. Uwais sak! Fari sol bai debo komai a jikin Amrah ba. Hatta farcen yaron irin na Uwais ne.

Fahimah jin wata irin soyayyar jaririn ta yi, ko don kamanninsa da Uwais, ta kifa kai jikin Ammi tana kuka. Uwais na ta kira babu wadda ta iya amsa wayar sa. Ammi ta ce, Fahimah ta zauna ita da Talatu za su tafi da jaririn maigadi ya kira makwabta a yi masa sutura.

Ba su jima da tafiya ba aka gungura Amrah zuwa aminity. Da sauri Fahimah ta bi bayansu suka kwantar da Amraha kan gado suka yi mata duk abin da ya dace sanan suka fita.

Fahimah ta ja kujera daidai kan Amrah ta zauna. Tana karanta addu'a tana tofa mata. Ga karin jini ga na ruwa, tana da son haihuwa matuka, musamman da Uwais ya ce zai so 'ya'yansu ne fiye da son da yake yi wa kansa.... Amma in haka haihuwar ta ke lala - lala ta hakura. Lallai wannan shi ne kafa daya a duniya, kafa daya a lahira.

Ta tuno uban jinin da ta ga Amrah na zubarwa, wani matsanancin tsoro ya kara kamata. Tunda dai Allah ya taimake ta ba ta yi cikin ba, to ba za ta kara yarda ta yi abin yin cikin ba. Ta barwa Amrah Uwais su yi ta haihuwa, tarewar ma ta fasa ba za ta yi ba. Zata cigaba da zama da Ammin ta.

Wajejen karfe goma na safe Amrah ta bude idonta a hankali. Kafin idanunta su washe a dakin su sauka a kan jinin da ake kara mata. A lokacin ne ta fahimci a kan gadon asibiti ta ke. To me ya kawo ta asibiti ita da ta kwanta a gadon Fahimah za ta yi barci?

"Masha Allah, kin tashi Aunty Amrah? Bari in kira likita". Ta ji muryar Fahimah a gefenta.

Muryar da ta tado mata da ainahin dalilin zuwanta asibiti. Da sauri ta kai hannu kan cikinta ta ji wayam! Da azama ta yunkura za ta mike, daidai lokacin da likitan ya shigo, Fahima na biye da

shi. Da sauri ya maida ita kwance, ya ce, “Be careful Madam, akwai aiki a jikinki”. Sannan ya tambaye ta,

“Are you alright?”

Kai kawai ta gyada masa. Ta runtse ido da Fahimah ta zagayo gefen fuskarta, tana tambayar likita ko za a iya ba ta tea ta sha? Doctor ya ce, ta bari sai an jima, Nurse za ta zo ta ba ta da magani.

Tunda Amrah ta rufe ido ba ta kara budewa ba. Don ba ta son ganin Fahimah, ba kuma barci ta ke yi ba. Har zuwa lokacin da su Ammi suka dawo.

Ammi bata san Amrah ta farka ba ta tsaya tana gaya wa Fahimah har an binne yaron. Allah ya ba su wani mai albarka, Ya bai wa iyayensa dangana. Shi ma Uwais din yana hanya gobe duk da bai gama abin da ya kai shi ba.

Wasu dumammun hawaye suka biyo ta gefen idanun Amrah, Dan ta ya koma, duk wannan wahalar da ta ci akan rainon cikin, duk a dalilin bakin cikin Fahimah da Uwais? Ko Uwaisu ne autan maza ta hakura da shi yau, in ba haka ba bakin cikinsa shi zai yi ajalin ta.

Ta soma tunanin hanyar da za ta bi ta tsere kafin Uwais ya zo ya tadda ita. To amma da wanne ido za ta koma wa iyayen ta???

Wannan tunanin ya sa Amrah fashewa kuka wiwi a fili. Su ba su san idonta biyu ba, kuma sun dauka kukan na rashin dan ta ne da ta yi. Su basu san abubuwan sun ma zuciyar ta yawa ba. Da wanne zata ji?

Ammi ta karasa ta kama hannunta tana ba ta baki. Ta ce, “Ki yi hakuri Amrah, insha Allahu mai ceton mu ne. Ba ki ganshi ba kamar Uwais ya yi khaki. Allah ya yi wa iyayen da suka rasa ‘ya’yansu suna kanana babban tanadi a ranar gobe. Kada ki yi bakin ciki, ki yi addu’ar Allah ya bada rayayye mai albarka,  kin ji”.

Amrah ko kallon Ammi ba ta yi ba, ta ci gaba da gunza kukanta. A ranta ta ce, duk abin da Uwais da Fahimah ke yi da sanin Ammi tunda ai a gabanta suke, and she is educated enough da za su yi irin wannan danyen aikin ba da saninta ba.

Me kuma za ta ce mata yanzu? Ai ta bar mata danta ke nan har abada ta aura wa farkarsa, ko su ci gaba da watsewar su.

Gaba daya sun kasa gane kan Amrah, tunda ta farko ta ki ci ta ki sha, sai kuka, sannan ta ki karbar lallashin Ammi.

Har dare suna tsaye a kanta suna lallami, amma ko uffan ba ta ce musu ba. Sai da Ammi ta koma ta kira babban likita ta ce ya bincike ta ko da wani abu da ke damunta daban, kada jininta ya hau.

Likita ya shigo, ya ce duk su ba shi wuri zai yi magana da Amrah. Ya ja kujera a gabanta ya zauna, ya ce, “Madam, may I know your problem? Na dauka ke musulma ce, kin san mutuwa tana kan kowa babba da yaro? Na dauka za ki yi tawakkali ki yi masa addu’a, ki roki Allah ya sake ba ki wani cikin gaggawa?”

Amrah na kuka ta ce, “Doctor ni farin ciki nake da Dan ya koma. Ko bakomai zai dandani irin bakin cikin da ya kunsa min. Tunda gashi nan a dalilin cin amanar da yayi min shima ya rasa abinda ya kallafawa rai.

Damuwata yanzu kawai yadda zan je Abuja. Ka taimaka min ka sallame ni a yau, kuma ka ba

ni aron wayarka in kira direbana ya zo ya dauke ni”.

Doctor ya ce, “Babbar magana. Ba zan iya sallamarki ba sai jibi, a ka’ida in aka yi wa mutum aiki sai bayan kwana uku ake iya sallamarsa shi ma in an tabbatar babu wata matsala da za ta biyo baya. Advisably ki bar ni in yi wa Mamanki bayani cewa kina son tafiya Abujan da zarar an sallame ki, na tabbata za ta fahimta ta kai ki da kanta…”.

Da sauri Amrah ta ce, “Doctor ba abin da ya hada ni da su, kuma in ba za ka taimaka min ba wallahi ko a kan iska sai na tafi".

Ta ci gaba da rusa kuka. Doctor ya rasa ya zai yi da ita, da ma kuma yana da lambar Uwais da suke magana wadda waccan likitar data karbi Amrah ta bashi da za su yi handing over, sai ya koma ofis ya kira shi, ya yi masa bayanin halin da matarsa ke ciki.

Uwais ya rasa inda zai tsoma ransa ya ji sanyi, ga booking dinsa ma an ce ba zai samu ba a goben sai bayan kwana uku, na goben bai yiwuwa saboda hazo. Da kyar ya iya ce da Doctor ya kula sosai kada ya barta ta fita, har zuwa kwana ukun, wato ranar sallamar ta, zai turo matar Yayanta ta tafi da ita, ya tabbata za ta yarda ta bi ta.

Daga nan ya kira Jabeer, a yadda Jabeer ya ji muryar Uwais ya tabbata ba lafiya ba. Ya ce, “Jabeer, I donno from where to start, don ko kai ba za ka yi min uzuri ba balle Amrah. Amma wallahi ka yarda da ni ina da niyyar gaya mata ne da zarar na dawo, don in samu ta haihu lafiya. Sai kaddara ta riga fata. Yau ga kuskurena da rashin jin shawarar mahaifiya sun jawo na yi asarar babyna”.

Jabeer ya ce, “Hasbunallahu wa ni’imal wakeel, me ya faru haka Uwais?”

Uwais ya share zufar da ke yankowa daga goshinsa, ya kwashe komai ya gaya wa Jabeer, ya kare zancensa da cewa, “I never take it serious, (auren sa da Fahimah), kuma tunda na mallaki Amrah ban kara waiwayar zancen Fahimah ba.

Na yi duk iya kokarina a kan Amrah ta fahimce ni ban iya rayuwa babu macen aure, ta dawo B.U.K mu ci gaba da rayuwarmu. Amrah ta ki fahimtata da gangan, ta sa kafa ta yi tafiyarta Malaysia ta bar ni. As a man like me na san za ka fahimci halin da na kasance kuma na san ina da wata matar.

Amma wallahi Jabeer ban taba tunanin auren zai je ko’ina ba shi ya sa na dauki lokaci ban gaya wa Amrah ba, sai kuma ga ciki ta samu mai matsaloli, sai na kara jinkirtawa da niyyar zuwa ta sauka.

Ban san ya aka yi Amrah ta zo gidanmu ba, har dakin Fahimah, har wayar Fahimah ta je hannunta. Daga nan komai ya lalace wanda I’m sure shi ne sanadin nakudarta.

I’m sorry Jabeer, wallahi ban yi da niyya ba, haka Allah ya nufa. Jabeer babyna da na kallafa wa rai ya zo ba rai, sannan Amrah na can ta tubure musu Abuja za ta koma. Bayan already na yi booking ina tafe in three days”.

Jabeer ma ransa ya baci sosai, amma sai ya yi hali na dattaku, ya ce, “Ka yi babban kuskure Uwais, kuma magabatanka ma sun yi kuskure tun a wajen neman auren Amrah ya kamata ku gabatar da wannan maganar, in ya so in yin yin, in barin-barin. Amma yanzu ka bata goma daya ba ta gyaru ba. Don ka san Daddy ba wai yana farin ciki da aurenku ba ne don dai ya ga Amrah na so ne ya hakura.

Don haka ni ban isa in rike Amrah a gidana ba tare da iyayen mu sun ji zancen nan ba, don

Murjanatu ba ta taba haihuwa ba, ba ta san ya za ta yi da Amrah ba. Don haka in an sallame ta zan je in dauke ta a asibitin mu wuce Abuja".

A sautin muryar jabeer Uwais ya tsinkayi bacin rai sosai, don dai yana kokarin dannewa ne. Babban bacin ran Jabeer wai a ce har shi bai gaya wa yana da wata matar bayan Amrah ba? Duk yadda suke da shi, ai zai iya gaya masa ma tun lokacin auren in ya so ya roke shi ya rufa asiri. Wannan itace abota ta hakika. Amma ina? A lokacin idon Uwais ya rufe da son mallakar Amrah anyhow.

Don haka yanzu kam yana bayan kowanne hukunci Amrah za ta yanke wa aurenta da Uwais don tana matukar sonsa, kuma ya yi betraying dinta a magana ta gaskiya.

Shi ya sa har kullum mota suke kuka da maza a kan rashin amanar soyayya, da gaske ne su maza ba su da tabbas in dai a kan mace ne. Amma why Uwais? Mutumin da ya ke yi wa kallon wanda ya fi kowa son Amrah? (in kina tunanin namiji na da tabbas a kanki to ki daina- Takori).

A yadda suka yi sallama da Jabeer a wayar ma duk da yana kokarin dannewa ya fahimci ransa ya baci sosai a matsayinsa na shakikin Amrah. To ina ga iyayenta da ita kanta?

Bai dora neman aurensa a bisa tafarki na gaskiya ba tun farko don haka he must try to be a man, ya yi dammarar facing every challenge da zai biyo baya kawai.

Duk maganganun da suke yi a kunnen Murjanatu wadda ke zaune a gefen sa. Bayan sun gama ta dubi mijinta sai huci yake yi. Murjanatu akwai ilmi, hankali da kyakkyawan tunani, don haka ta ce da mijinta Jabeer.

"Uwais abokinka ne na gaskiya wanda ya kamata a ce cikin kowanne hali ka tsaya tare da shi. Kada ka bi bayan kanwarka ka manta da darajar abokan taka. A halin yanzu he needs your support most. Kada ka manta mahaifyarsa ce ta yi masa umarnin auren yarinyar nan, kuma ita ke rikonta sannan ta ce in bai aure ta ba, Amran ma ba zai aura ba. I'm sure dalilin shi na amincewa kenan. Wato tsoron rasa auren Amrah.

Kamar yadda ya ce din ne if you are in his shoe, ya za ka yi? Za ka yi zina ne tunda ita ta ki zama, ko ko za ka tafi ga ajiyayyen halalinka da ke gefe?"

Jabeer bai ce mata komai ba, amma yanayin fuskarsa ya nuna sassauci.

"Ki tashi mu je mu ga halin da ta ke ciki, ya ce tana asibitin standard".

Murjanatu ta dauko mayafinta ta bi bayansa, domin tuni shi har ya kai waje. Babbar damuwarsa ya san laifin Uwais shi ma sai ya shafe shi a wurin Daddy, tunda dai komai ma shi ne sila.

Da tambayar sunan patient wadda aka kawo jiya, ta haihu dan ba rai Jabeer da Murjanatu suka dangana da dakin da su Fahimah suke.

Suna tsaye a kan Amrah ita da Ammi, Fahimah rike da kofin shayi mai kauri, Ammi rike da plate din kwai da dafaffiyar hanta da Talatu ta kawo suna ta aikin lallashinta a kan ta ci, Amrah ko idonta ta ki budewa balle ta dube su, abin da ya soma hassala Ammi don dai ita ba ta san laifin da suka yi mata ba, amma Fahimah ta fara shan jinin jikinta.

Sallamar Jabeer da matarsa a dakin ya sa Amrah ware dukkan idanunta. Sannan ta yunkura da karfi za ta tashi, Murjanatu ta yi gaggawar rike ta ta maida ta kwance tana fadin, "Oh no

Amrah. Ki bari ki samu lafiya, ga ni na zo. Sannu kin ji? And we're going to Abuja together".

Amrah ta ji hankalinta ya kwanta, sai ajiyar zuciya ta ke yi, ta kuma daina kukan. Abin da ya daure wa Ammi kai, wato su ne ba ta son gani, to me suka yi mata ban da abun arziki? Ko tana zargin su suka kashe dan Uwais da hannun su?

Murjanatu ta juya tana gaida Ammi, kallo daya ta yi wa Fahimah ta gane ita ce matar Uwais. Class din yarinyar ya isa. And her black skin is expensive and radiant a cikin mata. Sai ta ji kwarai itama tana taya Amrah kishi da gaske.

Kishi da wannan zukekiyar black beauty ai sai jarumar mace mai karfin zuciya, wanda ta tabbata Amrah ba ta daga cikinsu.

Har dare Murjanatu na tare da su, ita ta sa Amrah ta karbi shayi ta sha. Abin da ya kara tayar wa Fahimah hankali shi ne, yadda tunda Amrah ta farka ta ki ko da duban inda ta ke.

Wannan ya tabbatar mata da kyar in wani bai lalata al'amarin ba (ya riga Uwais gaya wa Amrah) wanda shi ne sanadin nakudarta da wannan fushin da ta ke musu har Ammi.

Duk sai ta ji jikinta ya yi sanyi, don haka ta janye jiki daga inda Amrah ta ke. Daga baya ma ganin Murjanatu na nan ta ce da Ammi za ta koma gida ta yi wanka sai dare za ta dawo ta kwana. Ammi ta ce, Murjanatu ta tambayi Amrah me ta ke so a kawo mata da daddare?

Amrah ta tsuke baki ta ki cewa komai.

Ammi sai da ta kai zuciyarta nesa, amma da ita ma tafiya ta yi niyyar yi tare da Fahimah, amma ta taushi zuciyarta ta zauna. Ita kanta Murjanatu ba ta ji dadin wannan hali da Amrah ke nuna wa uwar mijinta ba. Amma Ammin tana wajen ba ta tashi ba, don haka ba dama ta yi mata fada.

Da Murjanatu ta tashi tafiya bayan magriba da Jabeer ya zo daukarta, Amrah tuburewa ta yi ba ta yarda Murjanatu ta tafi ba, sai dai ta kwana da sassafe su wuce Abuja ko Doctor bai sallame ta ba.

Kunya kamar ta kashe Murjanatu, don a gaban Ammi Amrah ta fadi maganarta kanta tsaye. Ita ma Ammin tun daga nan ta sha jinin jikinta cewa, abin da ta ke guje wa Uwais tuntuni ya faru. Wani munafikin ya yi masa riga malam masallaci.

Sai ba ta ga laifin Amrah ba, domin laifi guda har da rabi Uwais ya yi mata. To amma ita kam babu ruwanta, wanda ya ja ruwa shi ruwa kan doka. Ba yadda bata yi da shi ba akan ya fada mata tun farko ya ki.

Dole Murjanatu ta kwana, Fahimah kuma da ta koma gida ta dauki wayarta a inda Amrah ta yasar da ita, sai ta duba missed calls dinta. A nan ta ga received call na Uwais da sha biyun dare kamar lokacin da yake kiranta kullum don yin midnight call.

Ta tuna a inda ta bar wayar, da kuma barci da ya dauke ta da wuri. May be Uwais ya kira, Amrah ta dauka, shi kuma ya yi barambaramarsa da ya saba. Mutumin da in ya soma sakin romantic zance sai ta rasa inda za ta sanya kanta don kunya.

"Hasbunallahu wa ni'imal wakeel".

Fahimah ta fada a fili, ta zauna gefen gado ta dafe kanta.

Wannan ne ya sa ta kasa komawa asibitin da daddare. Ta ma kashe wayar don kar Ammi ta kira ta ce me ya sa ba ta dawo ba. Shi ma Uwais yau ba ta so ya kira ta. Kowa ya je ya ji da damuwarsa shi kadai.

Ko barci ta kasa, sai kawai ta dasa nafilfili a tsayin daren baki dayansa. Takamaimai ba ta san me ta ke roka ba. Ko me ye bukatarta? Ban da Allah ya kawo daidaiton zukata cikin

al'amarin, domin ba za ta so auren Amrah ya mutu a kan nata ba. Ciwon 'ya mace na 'ya mace ne, ko ita aka yi wa haka duk son da ta ke wa Uwais sai ta hukunta shi, balle Amrah da ta dauki dukkan yardar duniya ta ba shi.

Ita da ma a philosophy dinta babu sakankancewa a kan cewa namiji nata ne ita kadai. Ta sa a ranta bayan Amrah, Uwais na da damar da zai karo mata biyu, don haka ba ta taba yaudarar kanta ba kamar yadda Amrah ta dauka. To ina batun da ta ke yi mata a baya na cewa ta auri Uwais? Ashe dama duk a baki ne bai je har zuci ba zafin laulayi ne, lol? Ita kam tun daga wancan lokacin ne ta ji ta kara son Amrah, duk da hakan bai hana ta jin kishinta lokaci zuwa lokaci ba.

Washegari da safe bayan ta yi sallar asubah da wuri ta shige kitchen ta shirya abin da ta tabbatar Amrah za ta iya ci, da wanda su Ammi za su ci, sannan ta dauko basket din zuwa waje da zummar zuwa bakin titi ta hau adaidaita zuwa asibiti.

Tana fitowa harabar gidan motar Ammi na shigowa. Don haka ta ja tunga ta tsaya har Ammi ta yi parking a inda ta ke ajiye motar kullum. Fahimah ta karasa ta karbi hand bag din hannunta suka rankaya zuwa ciki. Tana fadin,

"Da ba ki wahalar da kanki ba sun tafi Abuja tun dazu, kuma kin kama kin kashe waya balle in gaya miki. Ni yau na ga abin da ya ishe ni, kishi hauka ne da za ki sabi hanyar Abuja da sabon CS a jikinki?"

"Hasashena ya tabbata!" Fahimah ta fada a ranta.

Jiki a sanyaye ta maida basket din kitchen ta koma daki. Ta kunna wayarta kenan kiran Uwais ya shigo, da sauri ta sake kashewa don ba ta da courage na cewa komai.

Amma sai ga Ammi ta biyo ta da tata wayar har dakin, "Fahimah, don me za ki ki amsa wayar mijinki saboda wata can ta yi fushi da ku? Maza karbi ki yi masa ta'aziyyar rashin da ya yi, ai shi ya ja wa kansa da ya bi maganata tun farko, da yanzu hankalinsa a kwance. Yana bukatar mai lallashin sa, maza karbi wayar nan kamin ki bata min rai".

Fahimah ta karbi wayar. Ammi ta juya ta fita.

"Fah-himah, are you there?"

Muryar Yaya Uwais, ta karya zuciyar Fahimah ba ta taba jinsa ya yi magana a wanan yanayin ba.

A hankali ta ce, "Ya Uwais, I'm sorry… for all the inconveniences, ka zo ka dauke ni mu je mu yo bikon Aunty Amrah".

Murmushi ya yi mai sauti, ya ce,

"Ba tafiyarta ce damuwata ba Fahhimah. Yadda na zama silar rasa baby dina. Fahimah I love babies, and I lost one. Ban san kuma yaushe Allah zai sake ba ni wani ba".

"Soon insha Allah…". In ji Faheemah, sannan ta sassauta murya ta ce, "Ina maka ta'aziyya Ya Uwais, Allah ya sa mai ceton mu ne".

Ya lumshe ido ya ce, "Na gode Fah-himah, amma ya aka yi wayarki ta je hannun ta?"

"I don't actually know. Kawai na farka na ganta a kaina cikin jini".

Ta fada masa duk yadda aka yi suka ga Amrah ta zo ba zato ba tsammani da yadda ta kai ta dakinta don su kwana tare.

Uwais ya yi ajiyar zuciya, ya ce Allah ya riga ya tsara za a yi hakan, amma na yi niyyar gaya mata da zarar na dawo. Ya rage nata ta dawo ko ta yi hukuncin duk da ta ga dama".

"A'ah Ya Uwais ba za a yi haka ba, kai ka yi laifi dole ka zage kwanji wajen bada hakuri har sai ta sauko. Ni ba bakuwar zafi ba ce ko guda uku ne ka karo……...".

Muryar Uwais wani iri ya ce, "Sabida ke ba kya kishina ko? Ko sabida ba ki sona Fah-himah?"

Dariya ta yi, ta ce, "In ka ji So, to daya kenan. So, so, so i love you so much. Ina son ka sau malala gashin tunkiya…...".

Uwais ya ce, "Ina nan tafe jibi in gani practically, ban yarda da wannan malalar ba. Da Ammi za ta yarda ma tare za mu koma in karasa sauran satittikan da suka rage min, ko outside masaukin mu sai in kama gida, don cikin mu babu wanda ya zo da mata".

Fahimah ta ce, "Sai ya Uwais?"

"Yeah, Uwais daban yake kamar yadda matarshi Fahhimah ta ke daban a cikin mata".

Murmushi Fahimah ta ke from ear to ear duk wani tension ya barta. Ta dauka yana cikin mummunar damuwa MATAR SO ta daka borkono, sai ta ji sabanin hakan.

Sun dade suna hira kamar ba kudi Uwais ke narkarwa ba. Ya ce, akwai kyakkyawan albishir da zan muku ke da Ammi, amma sai na dawo. Now, kiss me a little ko na ji dan sanyi a zuciyata".

Tafukan hannunta ta kai ta rufe fuskarta.

"Ya Uwais!"

Shi ma ya ce, "Yaya Fahhimah, I LOVE YOU".

Fahimah kamar ta narke sabida yadda kalaman Uwais suka ratsa ta, suka tsirga har cikin ruhinta. Da yana kusa, kuma za ta iya, a wannan lokacin ba ta san wace irin runguma za ta yi masa ba.

"Zan ba ka babban kiss, amma sai ka dawo".

Fahimah ta samu kanta da fada ba tare da ta shirya ba, tana mai mamakin kanta.

"Are you sure?"

"Very sure Ya Uwais, Allah ya kawo ka lafya".

Zuciyar kowannensu wasai suka yi sallama.

****

ABUJA

A cikin mota a kan hanyarsu ta zuwa Abuja ba irin ban baki da lallashin da Aunty Murjanatu ba ta yi wa Amrah ba, amma Amrah ko sauraronta ba ta yi ba, ta yi rantsuwa ta gama auren Uwais ko da shi ne autan maza.

Sai karfe biyu suka isa gidan su Amrah a Apo, Mama sai ganinsu ta yi katsahan, Amrah babu katon ciki, sannan babu jariri. Itada ta kama hanya ta tafi ko kwana biyar ba'ayi ba. Mama ta ce, "Lafiya? Kin haihu ne? Ina dan?"

Amrah ta fada jikin Mama tana kuka. Wani irin kuka mai cin rai. Daidai lokacin da Aunty Wasila ta shigo da sallama don ita haka ta ke, kullum kafarta tana gidansu, ba ta zama gidan mijinta sam, da ta taso aiki sai ta zo ta rashe sai dare ta koma.

“A’ah Amrah kuma? Ke da ki ka tafi jiya ki ka ce ba za ki haihu wajenmu ba kada mu kashe miki da?”

Amrah ta kara sautin kukanta kamar za ta tsaga falon, ba ta ce komai ba. Sai Murjanatu ce ta yi wa Mama bayanin duk abin da ake ciki. Shi kuma Jabeer da ma tun shigowarsu falon Daddy ya wuce don ya same shi su tattauna.

Mama da Aunty Wasila kwafa suka yi, Aunty Wasila har da dariya, ji kake kyal-kyal-kyal. Suka ce, “Amrah Lailah matar Uwais Majnoon, how market?”

Amrah ta kara kuluwa fiye da wadda ta ke ciki, ta ce, “Duk da hakan dai na ji ina sonshi har gobe ya ya ranki? Ni boye min din da ya yi ne tun farko ya bata min rai. Amma yarinyar ba yau na santa ba, ba ta da matsala sam. I just cannot share my husband with anyone shi ya sa na yanke shawarar hakura da shi gaba daya”.

Mama ta ce, “Gantalalliya, a haka za ki kare cikin bacin ran namiji kuwa, wai har yanzu tana son kayanta. To don ubanki tashi ki koma inda ki ka fito, ba za ki kwana min a gida ba”.

Murjanatu ta ce, “A yi hakuri Mama, yanzu jego ne a gabanmu. Wanka za'ayi mata a gasa mata jiki don Allah a dama mata kunun kanwa a gasa mata nama da dan ruwa-ruwa”. Ta fada cikin lallashin surukarta.

Mama duk da haushin Amrah da ya kusa fasa mata zuciya, haka ta daure ta bi umarnin Murjanatu.

A can falon Daddy shi da Jabeer, kasancewar ranar lahadi ce yana gida, Daddy ya ce, “Lafiya na ganku haka hajaran-majaran da tsakar rana?”

Jabeer ya ce, “Mun kawo Amrah ne".

A fusace Alhaji Umar Dikko ya ce, “Uban me ta dawo ta yi mana? Ban ce kar ta sake ta dawo min gida ba? Ta je can wajen Uwaisun ta haihu, tunda ita ba ta san abin da ya kamata ba? Ana mata gata tana ganin ba a sonta".

Jabeer ya ce, “A yi hakuri Daddy, ta haihu yau kwana uku dan ya koma”.

Jikin Daddy sai kuma ya yi sanyi, don yana son Amrah sosai duk bacin ran da yake yi a kanta, ai don ya ginata ne. A sanyaye ya ce,

“Shi ne kuma ta dawo?”

Jabeer ya ce, “Akwai wata maganar bayan wannan’.

“Ina ji”. Ya fada a kagare.

“Eh to Daddy, Uwais ya yi wa Amrah laifi, wanda ya dace ku sani. Ashe tare aka daura auren Amrah da na wata ‘yar uwarsa a lokaci daya mu ba mu sani ba. Sai yanzu Amrah ta gane. And he confessed to me. But please Daddy take it easy na san Uwais is a brave husband zai iya zama dasu su duka kuma yana da halin da zai rike su, kuma daga yadda na fahimta mahaifiyarsa ce ta tursasa shi ya auri waccan din. Na tabbata zai kasance mai adalci a tsakaninsu".

Alhaji Umar Dikko bai san sanda ya kwada wa Jabeer ashariya ba, har yana zaburowa daga cikin kujerar sa, ya ce, “kun ci kaza-kazan ku kai da Uwaisun naka ku raba. Ya rike adalcinsa, ni ma in rike ‘ya ta. Ni za a raina wa hankali?

Nan wannan Balaraben kawun nasa kamar mutumin arziki da ya zo nema masa auren me ya sa bai gaya min gaskiya ba? Nawa Amrah ta ke da za a hada ta da kishiya ko ashirin fa ba ta kai ba, uwarta sai da ta shekara ashirin tare da ni na yi mata kishiya, balle a yi wa tawa ranar

nata auren.

Da ma auren ba wai ya gamshe ni ba ne. Na ga amrah na so ne, shiyasa na hakura aka yi. Amma ya yi da Umar Dikko dan Adamawa".

Ya fiddo wayarsa a take ya kira Uwais amma ba ta shiga, ya yi ya yi ya kasa samunsa. Sai ya juya ga Jabeer,

"Ba ni shi almuri a lambar da ku ke magana".

Jabeer ya soma bada hakuri, wata tsawa da ya daka masa ba shiri ya latso Uwais ya mika masa.

Uwais ya dauka Jabeer ne, don haka with much respect irin na wanda ya san ya yi laifi ya amsa. Sai muryar Babansu ya ji yana magana a matukar hasale.

"Kana magana da Umar Dikko Baban Amrah. Ina mai gargadinka da kada ka sake ka tako min gida, ka rubuta takardar sakin 'yata ka ba wa Jabeer ya kawo min, ka ji na gaya maka. In ba haka ba kuwa kotu ce za ta raba ni da kai, na rantse daga nan har kotun kolin Najeriya".

Ya kashe wayarsa ba tare da ya saurari Uwais ba, shima da ma bai da abin cewa, amma a fili ya sauke wayar sa, ya ce,

"Me ya yi zafi???"

Don so yana son Amrah har gobe, don she's his first love. Wadda ya fara mallaka wa ragamar zuciyarsa ya ba ta dukkan so da kauna. Amma duk abun mutuncin da zai hada da cin zarafi, to fa Uwais ba ya daukarsa.

Ya yanke shawarar rabuwa da Amrah cikin wani hali na kaka-ni-kayi. Kafin Alh. Dikko ya kai ga taba mutuncin sa. Ya gama gane iyayen Amrah ba su son aurensu kaddara da rabo ne kawai ya kaddara auren. Ita ma Amran fama yake da ita a kan karan-kanta don ba ta dauke shi a bakin komai ba. Hakkokinsa na aure kuwa a gantale suke yawo.

Ammi ta yi gaskiya da ta ce, kyal-kyal banza ya daina dibanka. Halin mutum shi ne yake sa wa a so shi ba nasaba ko zubin halitta ba. Amrah ga nasaba ga zubin halitta, amma ta rasa iyaye masu dattaku, nasaba da asali ba ta yi amfani ba anan.

'FAH-HIMAH!'.

Sunanta ya fado a ransa yana daga kwance. Ya wani irin lumshe idanunsa.

"Ita ko kara ya saka ya ce kada ta tsallaka ba za ta ko doshi hanyar ba. Ga iya soyayya in stylish. Komai cikin class da sanyin rai hadi da girmamawa. Ba ta da wayewa kamar Amrah, amma ta fi daidai da rayuwarsa. Tunda kuwa idan ya yi umarni za a bi shi, idan ya yi hukunci shi ne abin bi.

Me kuma yake nema a diya mace wanda bai samu a Fah-himah ba? Ya yarda Fahimah kyautar mahaifiya ce, kuma kyautar Allah a gare shi. Amrah kuma iznah ce kuma jarrabi a gare shi, duk son da yake mata da ita ma wanda ta ke masa rabuwarsu ita ce mafi alkhairi, domin zukata sun riga sun baci, ko an koma za a yi ta ganin juna da tsohon tabo ne.

Sannan upbringing na gidan su Amrah bai yi daidai da wanda yake fata wa 'ya'yansa ba. Fahimah ita ce daidai da shi, daidai da komai nasa.

Sun samu tarbiyyah iri daya, raino da upbringing iri daya, wanda yake fatan 'ya'yansa ma su taso a cikinsa…...

A bisa wadannan dalilan da ma wasu da dama, Uwais ya yanke shawarar rubuta wa Amrah

saki ba tare da ya yi shawara da kowa ba, daga Ammi har Fahimah don ya san cikinsu babu wadda za ta goyi bayan haka.

Bai baro Switzerland ba sai da rubutacciyar takardar sakin Amrah a cikin takardunsa.

****

Yau Uwais zai sauka a Kanon Dabo, don haka Ammi, Fahimah da Talatu kowacce tana tsaye a kan kafafunta tun safe. Yau kwanaki uku ke nan Ammi ba ta komai sai gyaran Fahimah da kayan mata masu inganci wanda a baya ba ta samu damar hakan ba.

Musamman ta yi wa Hajiya Asabe waya, ta ce ta kawo gudunmawa, gobe 'yarta za ta tare. Hajiya Asabe a ranar ta zo da babban shirinta har da dafaffiyar kazarta cikin romon maganinsu na Sokotawan usli.

Tun jiya Ammi ke ciyar da Fahimah nau'i-nau'in abin da zai kara ni'imtata, ya bambanta da sauran mata a wurin Uwais ko ya daina yo mata kwashe-kwashen 'ya'yan masu kudi (ta bakinta), wadanda ba su san mutunci ba.

Fahimah ba ta san amfanin abubuwan da Ammi ke ta dirka mata ba, amma tunda dadi gare su a baki ba ta da matsala da su. Sai a daren ranar ana i gobe zai dawo ne da ta shiga toilet don yin wanka kafin ta kwanta, ta ji jikinta gaba daya ya sauya, tafi-tafi ta ji ba wanda ta ke son bude ido ta gani sai Uwais domin gaba daya Ammi da Hajiya Asabe sun rikita hormones dinta.

Don haka tana fitowa daga wanka yau tun kafin lokacin hirarsu ya yi ita ta kira shi da kanta, Uwais na dauka ya ce,

"Anything special for  Uwais?"

Ta yi ajiyar zuciya mai nauyi, ta ce, "Ya Uwais, yaushe za ka dawo ne?"

"Gaya min tukunna, mene ne damuwar?"

Nan Fahimah ta hau kame-kame, "Ba wani abu fa Uwaisu- Uwaisunmu ni da yayata Amrah… I just want to see you, it is almost 70days ban sanya ka a idanuna".

Uwais ya ce, "Kin ma fadi gaskiya za ki yi bayani dalla-dallah in na iso domin Fahimah na tara da yawa.... only Fahimah can treat my unnamed illness".

Fahimah ta kai tafukanta ta rufe fuska tamkar Uwais yana ganinta. Da sauri ta kashe wayarta bayan ta ce, "Ya Uwais I'm not a doctor". Ba ta karasa jin me yake cewa ba ta kashe sabida yadda muryarsa ta saukar mata da wata irin kasala.

Sallamarsu ta daren jiya ke nan.

Kafin su gama aikin abinci ita da Talatu, Ammi ta yi kiranta. Tana zuwa dakinta ta ce, "Bar aikin nan wa Talatu, ki zo ki yi wanka da ruwan turaren nan, in kin fito ki zo ki yi tsugunno a kan wannan turaren, sannan ki saka kayanki".

Fahimah ta bi umarnin Ammi. Da ta gama ita da kanta sunsuna kanta ta hau yi sabida dadin kamshin da jikinta ke mata. Ta rasa ina Ammi ta samo wadannan mayatattun traditional turarukan.

Fahimah ta shirya cikin wani pink voyel wanda aka yi wa aikin dutse mai matukar kyau da tsari, babbar riga ce Senegales, Ammi ta ce ita za ta je ta dauko Uwais daga airport anjima, ita ba ta jin dadi, ba za ta iya tuki ba.

Duk da hannunta ba wai ya fada da tukin ba ne, wani zubin Ammi tana ba ta sai ta makala mata learner.

A shagwabe Fahimah ta ce, “Ammi gaskiya ni ba zan iya zuwa dauko Yaya Uwais ba, wallahi Ammi kunya nake ji”.

Ammi ta yi banza da ita ta ci gaba da shan shayinta, daga bisani ta ce, “To a barshi a can, kada a dauko shin, asarar wa? In don ta Safeeyyah-Basudaniyyah ne tana da ‘yarta, wata ce za ta yi asarar miji”.

Dariya fahimah ta yi don in Ammi ta so raha kamar kakarta ta ke komawa.

Ta dade a gaban madubi (dressing mirrow) tana kalmasa daurin kallabi, ta yi ta kwance ta sake daurawa, ta rasa wanne za ta bar wa Ya Uwais ya gani ya san cewa kwalliyar yau musamman don shi aka yi. Sai da Ammi ta kwala mata kira cewa lokaci ya kure, sannan ta hakura ta fita, bayan ta feshe jikinta da turaren oud midnight ta cakuda da (cerruti) ta yafa yalwataccen gyalen da ya shiga lightly da kayan jikinta, sannan ta fito.

“Na fito Ammi sai mun dawo”.

“Sai ki hanzarta, it’s almost past 8 now”.

Fahimah tuki ta ke a hankali ba ta gudu, sannan ba ta hawa tsakiyar titi da gani dai za ka san ‘yar koyo ce.

Tun daga ‘Yankaba har airport sabida lattin da ta yi tuni jirgin su Uwais ya yi landing suna can suna kokarin fitar da kayayyakinsu.

Ta tsaya daga can gefe, idanunta a kan kofar fitowarsu, yadda duk mai fitowa sai ta ga fuskarsa. Ba ta yi tsayuwar mintuna ashirin ba ta hango shi yana tahowa sabe da jakarsa. Ya maka bakin glass (GUCCI) a idanunsa.

Ba don ta yi masa farin sani ba, sama da shekaru sha takwas da ko kusa ba za ta gane shi ba. Domin kyawun da ilhamar sun ninka na baya, kasar Switzerland ga dukkan alamu ta gama karbarsa. Farar fatar nan ta yi luf! Sassalkar gashi ya kwanta a gefe da gefen fuskar wanda a baya ba ya barinsa bai aske ba. Sai ya koma Balarabensa sak da sirkin rayuwar kasar sanyi.

Ta gabanta ya gifta ba tare da ya gane ta ba. Sai kawai ta bi shi a baya. Har suka fita daga reception. Ya duba agogon (swatch - blustery) da ke daure a damtsen hannunsa yana kallon hanyar da jama’a ke bi. Kamar daga sama ya ji muryar Fahimah a bayansa.

“Maraba, lale, Ya Uwais!

Na kara baki ko akan nawa, shi ya sa ba ka gane ni ba?”

Da sauri ya juyo cikin wani irin yanayi, “Fah-himah, ke ce da kanki ki ka zo daukana? Wow! Lucky me’. Ya sa hanun damansa ya janyo ta barin damansa, daya hannun rike da bakar jakarsa. Kunya ta kama Fahimah, ta soma kokarin zamewa don ga mutane nan birjik suna wucewa, wasu suna shigowa. Ya ki ba ta damar hakan, domin kuwa ya rike ta gam-gam, suka zama kamar madara da bombita (black & white) suna taku tamkar ba su so, zuwa inda ta ajiye motar Ammi.

Ya bude booth ya sanya jakar hannunsa, sannan ya ce, “Ba ni makullin, ban shirya mutuwa yanzu ba da zan hau tukin ki. Ban dauki bakaken ‘ya’yana ba masu yi min addu’a? Ammi wane ganganci ya sa ta ba ki mota? Anyway, ni ta taimake ni cikin dimbin alfarmominta da ba sa karewa a gare ni”.

Ya karbi mukullin daga hannun Fahimah, ya bude mata gidan gaba ta fara shiga, sannan ya zagaya ya shiga ya zauna. Yadda yake treating dinta like a queen wajen shiga motar kadai abun ka tsaya ka kalla ne.

Maimakon ta ga sun dauki hanyar 'Yankaba sai ta ga Uwais ya karkata kan motar ya dauki hanyar Sultan Road. Suna tafe a motar yana satar kallonta yana fadin, "Fah-himah kin kara yin baki, amma kin kara yin fresh, in ji dai ba aikin wahala ki ke yi ba? Kodayake ko zirga-zirgar makaranta cikin ranar kasar Nigeria ya isa ya sa dalibi duhu".

Fahimah ta ce, "Umh, ina muka nufa ne Ya Uwais?"

Ya ce, "Inda ya kamata masoya kuma ma'aurata su samu privacy, kafin mu je ana kulle min mata ana saka min ka'idodi".

Fahimah ta gintse fuska ta ce, "Da wa ka ke kenan? Ammin?"

Ya ce, "Akwai mai rike min mata ne bayan ita da zan kyale shi yana abin da ya ga dama idan ba ita ba?"

Fahimah ta marairaice fuska tace, "Ni dai babu ruwana Ya Uwais, mu wuce gida don Allah. Ammi na can na jira, ta tanadar maka abinci, in ta ga mun dade me za mu ce mata?"

Uwais ya wani irin juyo ya dube ta yana shigar da sexy eyes dinsa can ciki, ya ce, "Akwai abincin da ya kai black wife dina dadi ne? Ki bar ni in mori kuruciyata kafin furfura ta zo 'ya'ya su cika gida su hana ni sakewa".

Ya karasa fada ta hanyar sanya hannun damansa ya rungumo ta gaba daya, saura kadan sitiyarin motar ya kufce masa. Fahimah ta zaro ido tana fadin.

"Ya Uwais kada ka zubar da mu ba mu ajiye wa Ammi 'ya'yan da ta ke buri ba".

Maganar Fahimah ba karamin dadi ta yi wa Uwais ba. Ya kara kankame ta da hannu guda yana tuki da dayan cikin gwaninta har suka zo gidan sa.

Maigadi yana nan don Uwais ba ya wasa da hakkinsa da extra ihsani. Suna zuwa ya zo da gudu ya bude musu yana ta faman sannu da zuwa wa Uwais, Fahimah ta yi gingirin a cikin mota ta ki ko motsi bayan Uwais ya kashe motar ya bude mata kofa.

"Fito mana my sweet 16? Ko sai an ja min ajin ne yadda aka saba? Kiyi a hankali kada ya tsinke don na kusa hango ta uku"

Fahimah ta tsuke baki ta tattare gira ta ce, "Ya Uwais! Ba zan shigar wa Amrah gida don ba ta nan ba, Ammi ta ce kowa da gidanta, ta ya ya za ka kawo ni gidanta?"

Uwais ya kankance ido cikin mamaki.

"Gidanta ko gidana? Nawa muka hada ni da ita muka sayi gidan? Tun muna shaidar juna ki fito, ko ki ga abun mamaki a cikin motar nan".

Amon muryarsa kadai Fahimah ta ji ta gane asalin Uwais dinta ne rigimamme, mara karbar uzuri kuma mara ragowa ta wannan bangaren. He will go far beyond abin da ya ce din in ta sake ta ki bin umarninsa, to kuwa maigadi zai sha kallo daga inda yake zaune. Motar Ammi farin gilashi kal gare ta.

Kafa a mace ta zuro ta kasa ta sauko tana turo baki tana kunkuni, "Haka kawai daga zuwanka sai rigima? Ba za ka bari mu gama gaisawa ba?"

Uwais ya sanya mukulli yana bude falon gidansa, ya ce.

"Akwai gaisuwar da ta fi wannan ma'ana ne?"

Ya karasa fadi ta hanyar janyo ta cikin falon da wata irin azama. Kamar yadda ta yi tsammani

farkon love making din Uwais hot and deep kisses ne a kullum, amma na yau ya fi na kullum domin a urunce yake sumabatarta a ko'ina, kusfa-kusfa yana yi yana kiran sunanta. Abin har sai da ya koma ba ta tsoro, domin ba ta taba ganinsa a cikin kwatankwacin irin wannan bukatuwar ba.

Tamkar bai taba kusantarta ba sai yau… ya ba ta dukkan soyayyarsa, ya ba ta dukkan amanarsa da sirrikansa wanda daga ita sai Ubangijinta sai shi suka sani. Wani hidden side ne na Uwais da ko Amrah ba ta taba gani ba don ba ya jin tsananin urge din da yake ji akan Amrah kamar a kan Fahimah.... wadda ta zo cikin takaitaccen lokaci ta gigita duniyarsa, ta canza ta, ta fahimtar da shi a baya ba soyayya yake ba, sha'awa ce ta kyawun halitta.

Duk da haka har gobe yana son Amrah, amma yana ganin rabuwar tasu ita ce mafi alkhairi a gare su baki daya. He will miss Amrah, amma yana da yakinin yanzu zai iya rayuwa ko babu ita. Infatuation dinsa a kanta kullum kara raguwa yake yi, anya haka Ammi ta barshi? Wane irin sirri ne haka tattare da Fahimarta?

Uwais ya kasa shiru, a bisa doguwar kujerar falonshi suke yana kanannade jikin Fahimah domin ta yi rantsuwa ba za ta hau gadon Amrah ba, dakinsa ma ba za ta shiga ba tunda kuwa Ammi ta raba tuntuni, duk wani hali na Ammi na tsayuwa a kan magana daya ya lura Fahimah ta dauke shi tsaf. Don haka ne ya sa shi ma ya hakura ya kyale ta suka sha soyayyarsu anan falon shi kamar babu gobe… a karshe Uwais bai yi mamaki ba da ya ji damshi a idanunsa, 'Hawaye yake yi ba tare da ya sani ba'. Fahimah ko a aljannah yana fatan a bar masa ita kadai a matsayin hurul eeninsa. Ya yafe 'yammatan aljannah.

"Ki yafe min Fahimah, hakika na yi kuskure a baya wanda yake hunting dina har gobe. Da zan iya da na maida bara-bana, na gyara all those inconveniences da na wanzar a tsakaninmu. Dana hadiye kalamai na na baya marasa dadi akan ki.

Watakila har in koma ga Ubangijina ba zan daina nadamar abin da na yi miki a baya ba. Ni dai na san a halin yanzu hukunta ni Ubangiji ke yi da hakkin ki, soyayyar ki nema ta ke ta kashe ni…".

Fahimah ta kai tausasan yatsunta ta toshe masa bakitana girgiza kai, cikin wata irin tattausar murya ta ke magana.

"Tashi mu tafi wajen Ammi haka Ya Uwais, ko ta ganka ta ji dadi a ranta itama. Na ga Uwais after 70days, na kasance cikin alfarmar Uwais after 70days ....in a way and manner da na tabbata wata diya mace 'yar uwata ba ta taba samu ba.

Idan na rike Uwais a raina bayan duka wannan ni'imar da Allah ya yi min ta mallaka min shi matsayin mijina uban 'ya'ya na, na zama mara godiyar Ubangiji.

Besides, an ce so hana ganin laifi Ya Uwais, ni fa ban taba jin haushinka ba, karewa ma komai ka ke yi burge ni ka ke yi. Rana daya ce na ji haushinka a rayuwata, ranar nan a Sudan…".

Da sauri shi ma ya toshe mata baki yana girgiza kai, "Kada ki tono abin da ya riga ya wuce, domin na tabbata alhakin wannan ranar ba nawa ba ne, naki ne. And i sincerely repented, so ni da ke duka masu laifi ne kuma tare za mu ke istigfari".

Let's go for another ........" Ya rada mata sauran maganar cikin kunnuwanta.

"Umh…" Fahimah ta iya cewa domin dadin bakin Uwais in yana son abin da yake so yawa gare shi, ba ta da ikon musantawa don bai ba ta damar hakan ba ma.

Ammi ba ta gansu ba sai karfe sha daya na dare. Fahimah sai baya-baya ta ke yi daga bayan Uwais da ganin ta ka ga mara gaskiya. Shi ko Uwais ko a jikinsa, karasawa ya yi da sassarfa ya rungume Ammi ya sumbaci goshinta. Da wannan damar Fahimah ta yi amfani ta gudu dakinta, ta barsu suna tasu soyayyar ta da da mahaifi. Har wata ajiyar zuciya ce ta kwace mata da ta ganta a dakinta. Ba tare da ta karbi query daga Ammi ba.

Ammi kuwa ba ta bi ta kan wannan ba, farin cikin ganin Uwais ya ishe ta. Sun gaisa sun sake gaisawa har da musabaha irin ta larabawa. Ta ce, “Uwais kamar ba kai ba, Switzerland ta amshe ka, ina fatan an yi nasarar duk abin da aka je nema?”

Uwais ya ce, “Nasara kam an same ta Ammi alhamdu lillah, ga sabon albishir da nake son yi muku, World Bank da muka je yin course dasu sun ba ni aiki tare da su a yanzu haka, na bar GT idan na dawo. Yanzun ban karasa ba saura sati 3 mu gama gabadaya, na ga cewa ya zama dole in zo in saita al’amuran gidana”.

Ammi ta ce, “Ina yi maka ta’aziyya Uwais, Allah ya sanyaya, Allah ya ba mu rayayye. Sannan sai ka kai zuciya nesa ka yi hakuri da Amrah, don kuwa laifi kan laifi ka yi mata. Don haka ka jure duk abin da za ka gani ko za ka ji daga gare ta ko iyayenta, tunda kai ne mai laifi”.

Uwais ya yi murmushi kawai ya mike, bai gaya wa Ammi abin da Alhaji Umar Dikko ya ce ba, na cewa in bai sako masa Amrah ba zai kai shi kotun koli. Da kuma hukuncin da zuciya ta kwashe shi ya yanke tun a lokacin ta sakin Ammi, yanzu haka takardar tana cikin kayansa, jira yake zuwa jibi in ya kara hutawa ya runtse ido ya kai wa Jabeer.

Yana addu’ar Allah ya sa kada rabuwarshi da Amrah ta yanke kyakkyawar alakar da ke tsakaninshi da Jabeer Dikko.

Wanka ya sake yi sannan ya sa farar shirt (Hilfiger) da wandon jeans dark blue ya fito falon jaye da akwatuna guda biyu.

Ya samu Ammi tana marking takardun dalibanta da medical glass a idanunta. Ta daga kyawawan idanunta ta dube shi tana murmushi.

“Sai ina kuma? Na ganka ka dau wanka ka janyo akwatuna? Ko bikon za a tafi cikin daren nan?”

Murmushi Uwais ya yi ya zauna a gefenta yana bude akwatunan, ya ce,

“Ammi bikon lafiya? Laifin me na yi da zan je biko? Na dauka bayan Amrah da Fahimah ina da damar kara guda biyu ba tare da na yi wa Ubangijina laifi ba?”

Ammi ta ce, “Haka ne, amma a al’adance ka yi laifi ba a addinance ba. Ni dai ban yi wa kowa cikinku laifi ba daga kai har Amrah domin kuwa auren Fahimah na sa aka fara daurawa, ban kuma ce wani cikinku ya boye zancen ba, don haka can ta matse muku kai da Amrahn. Amma ina so ka yi hakuri ka dauki girma ka amsa laifinka, sannan ka bada hakuri ta dawo dakinta. Kowa ta zauna a gidanta, ban yarda da hada muhalli ba”.

Uwais bai ce komai ba, ya rika fidda tsala-tsalan atamfofi, shaddodi da lesuka yana tulewa a gaban Ammi, ya ce, “Ammi ga tsarabarku. Sai ki zaba wa Fahhimah wanda zai dace da ita, I don’t know her favourite colours yet, kuma ban yi azancin tambayarta ba”.

Ammi farin cikinta ya fi gaban misali, “Allah ya albarkaci rayuwa Uwais. Amma ni tsohuwa me zan yi da wadannan kayan gayun? Na bar wa Fahimah bakidaya tunda tarewa za ta yi, ta je ta yi ta yi maka kwalliya da su’.

Murmushi ya yi ta sake cewa, “Ina na Amrah?”

Kamar ya ce mata, “She’s no longer Mrs   Shagari now”. Ya tuno halin Ammi na dattaku ba za ta bar shi ya bada takardar nan ba ko da za su kai shi kotun.

“Zan kai mata jibi in za ni, don gobe tun safe har dare in na fita ba zan dawo ba, zan maida hankali a kammala komai na gidan Fahhimah ta tare jibi, don tare za mu koma Switzerland tunda sun yi hutu, wata daya ne na gama gaba daya don a reshensu na Najeriya za'a ajiye mu. Kuma a garin Abuja ne, don haka zan nema wa Fahimah transfer zuwa (BAZE) tunda ta gama year 1”.

Ammi ta ce, “Hakan shi ne daidai, ni bana bayan miji na wani gari matarsa tana wani saboda kananan dalilai. Duk abin da zai zama dole ba a barshi a nemi alternative a zauna tare a nemi lahira. Tunda duk wani buri na duniya an gama samunshi, ilmi, career da aure na hakikah.

Yanzu sai shirin tarbar abokai da kawayen Ammi.

Sannan Uwais na aika takardar murabus daga aiki, idan kun dawo daga Switzerland kun nabba’a a permanent sabon muhallinku, ni kuma zan koma SUDAN gaba daya, a can zan karasa rayuwata. In kun haifa ku kai min Khartoum zan rike muku”.

Mu hadu a book 3 na karshe